Citation: Fallou Ngom (PI), Jennifer Yanco, Mustapha Hashim Kurfi, Garba Zakari, Daivi Rodima-Taylor, Babacar Dieng, and Rebecca Shereikis. 2022. "The Months and Seasons." https://sites.bu.edu/nehajami/the-four-languages/hausa/hausa-manuscripts/falke-1107-wattanin-ajamawa/.

# Watanni Ajamawa

[Page 1]

Bismi l-Lāhi al-Raḥmāni al-Raḥīm

Ṣalla l-Lāhu ʿalā l-nabiyyi l-Karīm

Na gode Wanda yai fuɗun fasloli

Ga zamani suke wuya, ji ƙauli

Mu sallama wa Ahmad, mai darajah

Da ƙasa har can bisa, babu mai ja

Na yi nufa za ni biɗa ḥisābī

Ga wāḥidun Rabbu mu san jawabi

Ka ji aboki, ga ni zan yin magana

Ta gaskiya ka shaida babu ga tana

Aboki zam ka tambayar kwanuka

Na shekara da za ta yi babu shakka

Shi ya sanadun ga shekara ʿarabiyyah

Koma faɗi shi sahahun ʿajamiyyah

Faɗi ni kai biɗassu kai don kassam

Kowanne fasali na cikin watan ajami

Shi ga lumba ɗayahhu kwanan rani

Suke shiga ḥaqīqatan; wa ka hani?

Gama Yuhin Yazzu shiga ta damuna

Agusshatu Yazzu da kaka hakana

Nuwambari Yawwu shiga ta ɗari

Ka ji abinda niffaɗi ya Qārī

Kowa ga Oktoba ya ga fasali mu faɗi

Kowanne kuwa na marabashi ba daɗi

Kowanne tisʿīna da guda jida mana

Ta'woza biyu ga Jabhah yazzam hakana

Kowanne faṣli shi riƙe guda bakwai

Na manzilah mu rarrabe su don akwai

[Page 2]

Far'u rani, damuna ga Hakatun

Sarfa da kaka ka ji ɗari Shaulatu

Daili da Ha-Kabiru rarrabesu

Shi yi Nahaju za ka yi ƙidansu

Ko ka yi tambaya ga Iʿtidālī

Su biyu na ka san su ba Ishgāli

Ji Iʿtidālī dudda Inqilābi

Ba su kawai zamne balle susaba

Da Jumbari dayya iaki Layāli

Su kwana arba'in ga na su Ḥāli

Ga Yulyuza bayya ake yin malka

Su kwana arba'in da babu shakka

Waninsu bakwai akwai su nan miyagu

Sukai daɗi ga Kufru nan su kango

Su ba ɗa Kahhu har guda Maris

Allah Shi tsarshemu garesu Inkis

Ka ji bakwai da sunka kas Adawa

Nufi da su ya cika babu wawa

Ga Yunyuhi kadda dare na Unsura

Babu ba inda ke shiga ga Qaddarā

Ka zo ga Afrilu ga Mā'u Nisa

Allah ciremu da shi; kar mu nisa